SCREENAFRICA™
BROADCAST, FILM, TV, COMMERCIALS, NEW MEDIA & TECHNOLOGY NEWS

AREWA24

**TASHAR AREWA24 ZATA FITAR DA JERIN SABABBIN SHIRYE-SHIRYENTA MASU KAYATARWA NA SHEKARAR 2016**

**19 JANAIRY, 2016 –** Domin samun ci gaba akan bunkasa da kuma farin jinin da AREWA24 ta samu a Arewacin Najeirya wanda ba'a taba samun irin sa a baya ba, tashar zata kaddamar da jerin sababbin shirye-shirye na harshen hausa masu nishdantarwa a Shekarar 2016. Tun farkon kafa tashar AREWA24, a watan Yunin shekarar 2014, gabatar da shirye-shiryen harshen Hausa masu kayatarwa wanda suke haska a'adun gargajiya sun kasance ginshikin ta. Tashar ta samu nasara wajen kaddamar da wasan kwaikwayonta na farko wato "DADIN KOWA" a wantan Fabrairu na shekarar 2015. Shirin Dadin kowa ya samu karbuwa sosai a gurin masu kallo kuma ya zama zakaran gwajin dafi a cikin wasan kwaikwayo na talbijin wanda aka rubuta da Hausa a Arewacin Najeriya.

Shirin Dadin Kowa, ya kai ga wata muhimmiyar gaba inda aka haska kashi na 50 na shirin a ranar 9 ga watan Janairun 2016. AREWA24 ta jaddada wannnan nasara ta hayar yin awa daya na musamman a shirin ta na Kundin Kannywood wanda ya shiga bayan fage domin tattaunawa da yan wasa, masu taimaka musu, marubata, masu daukar nauyi da ma masoyan wannan wasan kwaikwayo mai farin jini.

AREWA24 ta tanadi sababbin shirye-shirye wanda ake aiki a kansu domin haska wa a shekarar 2016, kuma sun hada da shiye-shiryen sati-sati da ma masu wasu salon. Tashar tana tsara shirye-shirye masu kayatarwa wanda zasu fadakar a kan Karya Doka, Cin Hanci da Rashawa da kuma wasanta na farko mai ban dariya, kuma zata kara duk wadannan shirye-shiryen a kan wasan kwaikwayonta na sati-sati wato Dadin Kowa.

Jami'ar Shirye-shirye Rakiya Usman ta ce "Nasarar da muka samu da shirin Dadin Kowa ta bamu damar kara gogewa wajen tsara shirye-shiye, kuma ta bamu karfin gwiwar tsara wasu sababbin shirye-shirye wanda zasu fi na baya". Ta kuma kara da cewa, "Dadin Kowa ya ciri tuta wajen inganci da rubutu mai kyau, da kuma hazaka. Masu kallo suna matukar kaunar shirin. Muna sa ran cewa, zamu ci gaba da kasancewa a sahun gaba wajen tsara shiye-shiyen harshen Hausa na Talabijin wanda babu irin su a Nahiyar Afirika a kowanne yare ta hanyar sababbin shirye-shiyen da muke tsarawa.

Sabon shiri na farko da za'a fara haskawa a AREWA24 a Shekarar 2016 shine, Shirin "Maganar Naira", wanda zai hada da sashin dakin shirye-shirye da kuma sashin mai ilimantarwa akan harkokin kasuwanci iri daban daban, tun daga kananan 'yan kasuwa zuwa masu aikin hannu da kuma shawarwari duk sati a kan harkar Bankuna, wacce zata taimaka wa jama'a ta fuskar dabarun yadda zasu sarrafa kudaden su.

Sauran sababbin shirye-shiryen da za'a haska sun hada da na Kade-kaden Gargajiya, shirin Salon kwalliya da kuma sabon shiri a kan Matasa, ("Manyan Gobe") wanda zai yi duba a kan al'amuran da suka shafi matasan Arewacin Najeriya.

"Babu tantama tashar AREWA24 ita ce jagaba wajen tsara shirye-shiye masu kayatarwa da 'Yan Arewacin Najeriya ke shiryawa don al'umar Arewacin Najeriya," inji Ms Usman. "Abu ne mai muhimmanci a ci gaba da samar wa masu kallon mu shirye-shirye masu inganci da Harshen Hausa, kuma su kasance masu ma'ana da kuma tasiri a rayuwar yau da kullum ta mutanen Arewacin Najeriya da iyalan su."

Ofishin shirye-shiryen AREWA24 dake Kano yana fitar da Shirye-shirye 13 nasa na kansa wanda suka hada da, Gari ya Waye, Kundin Kanywood, Tauraruwa da Matasa@360; da kuma shirye-shiye guda Biyu

Kano, Nigeria | The AREWA24 Channel, LLC | Lagos, Nigeria
1212 Market Street, Suite 200
San Francisco, CA 94102
*+1-415-561-4884*

da suka shafi harkar Wake-wake wanda fitaccen Mawakin nan kuma mai gabatar da shirye-shirye wato Nomis Gee yake gabatarwa, wato H Hip Hop da Top Ten. Sauran shirye-shiryen kuma sun hada da Taka Leda wanda shine babban shirin tashar ta fannin wasanni da kuma Alawar Yara shirin tashar Arewa24 na kananan yara.

**A kan AREWA24:** AREWA24 ita ce gidan Talabijin ta farko mai yada shirye-shiryenta 24/7 da harshen Hausa akan tauraron dan'adam, wacce kuma ake yin shirye-shiryen ta a gida domin haska Rayuwa, Al'adu, Dabi'u, Matasa, Kasuwanci, Fasaha, da kuma Nisadantar ga iyalan Arewacin Najeriya. Ku kama tashar AREWA24 a kyauta akan EUTELSAT 16A/16'0 (Frequency 10804, symbol rate 30000) ko kuma ACTV tasha ta 104. Abokanan huldar AREWA24 ta fannin yada shirye-shiye sun hada da Jordan Media City, Eutelsat da kuma Globecast. Jajircewar AREWA24 wajen yada shirye-shirye da Harshen Hausa ya cika wa masu jin Harshen Hausa a duk fadin Duniya wani gurbi, inda da yawansu suke amfani da shafin haska shirye-shiye ta yanar gizo na AREWA24.com a matsayin kafar da zasu ga al'adunsu dama na al'ummar duniya. Ana saka shirye-shiryen AREWA24 na kashin kanta a kowane sati a youtube.com/AREWA24channel, kuma tashar tana da alaka mai karfi da masu sadar wa da ita ta hanyar shafukanta na yanar gizo a AREWA24.com, facebook.com/Arewa24, da kuma twitter.com/AREWA24channel.

Domin karin bayani a tuntubi: info@arewa24.com.

Kano, Nigeria | The AREWA24 Channel, LLC | Lagos, Nigeria
1212 Market Street, Suite 200
San Francisco, CA 94102
*+1-415-561-4884*